Sanye take cikin doguwar rigar barci fari tar da adon yellow din furanni maras hayaniya ,mai taushin gaske ya lafe a jikinta ,saita saka doguwar hijabi iya gwuiwa a sama,ta dauko  tray din shayin larabawa a cikin dan butan shayi mai kyau, da d'an ficilin tambulan, da ada take had'a masa duk dare ,kafin ta kwanta ciwo,hannunta na dama yina kalmashe da casbiha dinta na lazimi,harta isa d'akin,saida tayi sallama ta nemi izini kafin ta shigo dakin sosai,yina kwance akan wata irin kujera faffad'a shiba gadoba ,kuma shi ba doguwar kujera ba ,bayida hannu d'aya,zuwa gabansa tayi ta russuna "Barka da hutawa jarumi ,sadaukin mijina ,Alfaharin yankinsa " murmushin yabawa ya jefeta dashi "Barka da isowa Gimbiya ta,a wajen mutane Nike da sarauta amma a wajen sahibata sarautata akeyi,bakiga yanda Nike jero kiraba ba qaqqautawa amma saida aka kintsa sannan aka ji qaina aka taho" "Afiwan ranka shi dad'e, a gafarceni" "bakya laifi amaryata tashi miko tebur ki aje kayan hannunki,don nasan in ban fansaba to a hakan zakiyi ta tsugunu" "Godiya Nike" ta mike ta miko wani dan ficilin tebur da yike a tsakanin kujera da kujera ta aje a gabansa ,tana zuba masa a dan tambulan din sannan tadan sunkuya ta mika masa "A gaisheda Gimbiya ta" ya fada ya kamota ya aje agefensa kafin ya tashi zaune,itakuma a hankali ta cire hijabin ta ninke a gefe,Kur6a d'aya yayiwa shayin ya lumshe ido "Hmm nasha kewar wannan shayin naki ,nayi cigiyar masana sirrin shayi suyimin irin wannan in biya amma na Gaza samu,Nagaisheda matata Aljannahta mai dubun basira Allah ya baki aljannah" "Nagode mijina da duk kokarin da ka yimun tsawon ciwona ,ka cancanci in maka jinjina samun miji na gari kamarka cikin wannan duniyar rabone ,Allah yabani dukkan damar da zan saka farinciki a iya tsawon zamanmu kar Allah ya bani ikon sa6a maka ,ka bani farinciki ka daukakani cikin tsararraki ka daga martabar zuciyata a burnin zuciyarka har ta azalzali bakinka da furtawa,batareda duba da matsayina na er ba kowaba,to dame zan iya saka maka?....saidai inyi maka addu'a Allah ya bayyanar maka da qwanka da zakayi Alfahari da ita a doron duniya kaima kace ga d'iyarka,,😭sosai ta e da kuka harda shesheka.
Bugun bayanta ya ringa yi a hankali bayan ya aje kofin shayin da ya zuqe
" Kukan ya Isah haka nan diyanah ,badon ki tunamun abunda ya faru a baya ko kiyi kuka na

kirakiba ,A'ah na kirakine don in maki kyakyawar Albishir ,ammafa sai bayan kin farantamun ,mun jiyarda juna farincikin da muka kwashe shekaru bamujiba....kinkosan yanda nayi kewarki diyanah,nakasa sabawa da rashin ki,duk wata d'iya mace ina fara tarayya da ita a shimfida zata zamar mun lami ,tamkar dusa,ke kadaice sha'awata akanki Alkalamina kad'ai yike jin ta6i harya motsa ba tareda An ta6asaba,kice Wanda tunanin ki kad'ai yikansa inyi inzali toh akan mene zaki rusamun tanajina,zo mujiyarda juna dad'i in nuna maki irin kewar da nayi naki"
Oh ni Oum Aphnan ,rubutu nikeyi ina nad'o maku rahoto ,banji ban gani sai girgiza kai,da dan murmushi a fuskata,tambaya ta shine waidama sarakuna suna da feelings? Ban auneba saidai naga mai martaba ya kwasa mun wata bahagon kallo daga inda Nike lafe aiko da gudu na kwasa takarduna nayi waje,na ciji yatsa,amma xakuga naci don sainadawo jin albishir na barku kushana kusha soyayya girmankune,ba tona sirri Allah ya nuna mana nasu su'adah wannan dolene ayi komai akan eyes dinmu😂💃

**
Ban samu zarafin dawowa ba sai wajen ukun dare,suna kwance cikin wani farin bargo maras nauyi, ta d'aura kanta akan kirjinsa suna magana k'asa k'asa yina shafa suman kanta.
"Kinaji na ko? Wato jiya su wambai da ciroma sunje gidan harsu shi yaron yusuf ashe ma dan gidan marigayine sule ngwandu mai rasuwa ,yanzu haka shine maiba mataimakin shugaban kasa shawara ,wato Ahamadu yaron mu, dan wajen ubaida yayata kina ciwo ya zama VP to shine suka so jin ta bakin en gidan nasu gameda 6atar yarinyar ,To a gaskiya andai shaida masu tabbas ba d'iyar sa bace a gidan marayu suka d'akko ta amma cikakken bayani yina wajen uwar Yusuf ,itakuma tana burnin tarayya taje jinyar d'an tan din ance tunda ta 6ace yake jinya,kinga wannan ya nuna yarinyar mu ta fada kyakyawar hannu kafin fad'awar wannan ibtila'in.
To ni yanzu shawarar da na yanke gobe zanyi kiran shi Ahmadun(yina nufin VP) zan shaida masa inason ganin yusuf tunda yina matsayin me basa shawarane,sai muje har gida a kwakwafesa kuma aji ta yanda akayi ta 6atan sai a San yanda za'a samota,don a jikina nikeji tabbas zamu samota nan kusa"
"Bakomai yalla6ai duk yanda kukayi daidai ne,yanzu su baba ciroman zasu tafi abujan wajen VP din ko ko yaya? Hmmm ikon Allah amadu dai da nasani ne ya zama VP? Koba Wanda ya ta6a rasa babynsa ba sanadiyyar matarsa?
" shifa Ashe dai qwalwarki ta dawo zam" dukule hannu tayi  ta sakin nasa dukan wasa.
Tasoma masa magana cikeda shagwa6a....

Hello🙋‍♀️Inada tambaya
Wai wannan wata masarauta ne,a wani gari take,sannan meye tarikhin wannan masarautan? Kuma dama VP da PA sunada alaqane da fadar ko ko gayyar masarautane kurum ,dasuka saba kar6an kowa nasu?

Muje zuwa a next episode
[7/27, 5:29 PM] Bamalli✌️: *JNS 2*

26-30

Dr.Khalid yina sauka daga airport wani sanyine ya lullu6esa yau dai gashi a Egypt kwana ya tashi a cikinta ,zaiga masoyiyarsa a koda yaushe yaso acikin Asibitin ,rataye yike da jakar baya a 6angaren hannunsa na hagu ,yina sanye cikin wasu ji6a ji6an kaya masu kamada track suit ash colour da ratsin fari ,yasaka cambas ma Ash da yarfin ja da fari, gashin kansa ya dauki sheqin mai ,an yankesu tsawo daidai  kufkuf dashi gwanin ban sha'awa,shine matashi na farko da naga ya Tara gashi kuma yayi masa kyau ,Wuyarsa rataye da wani roba kamar na headphones da yayi attaching da tabarau din idonsa ,Wanda gilas din ya ciresa a fuskarsa ya sakko masa a saman qirjinsa ,a nutse yike gangarowa zuwa inda zai samu taxi da zai kaisa asibitin,A tashin  fari bazaka ta6a kiransa JININ SARAUTA ba saidai kace masa matashi maiji da quruciya da tarin miskilanci,gaban taxi din airport din mai sunan airport d'in a baya ya hau,sukayi reverse suka fita filin jirgin.

Sanda ya shiga dakin bai tadda kowa ba sai Saudah dake yiwa su'adah alwala cikin wani roba mai fad'i tana bata labarin wani comedian kiddy buk da ta karanta ,ta apple dinta

"Aminiya akwai wata app wattpad suna saka littafin tsofaffin turawa masu yawan gaske ,inkin gama zan maki download din app din a tablet dinki da zan siyo maki yau in mu shiga suq(kasuwa) da ummah" "hmm lovely nagode, but still banida ra'ayin karanta Littafi Sam ,na d'auke sa 6ata lokacine,karki yaudara kanki wai ai na turancine,zaki qaru,aah duk d'aya ne,just muyi focusing a karatun ,there is yet time for that..." Qiyyy ya bud'e qofar yina sakar mata murmushin da akanta kad'ai yike iya yinsa ,karaf idonsu ya had'u "Oyoyo yayanahhhh" kallon tsaf ta bisa dashi kafin ta juyarda qwarar idonta a kan Su'adah cikin sigar tambaya da son qarin bayani "kin sanshi ne?" Jinjina mata kai kurum tayi,kafin tace "yayah qaraso daga ciki mana" murmushin jin dadin yanda ya ganta yayi kafin ya sako jikinsa duka ya samu kujeran d'ayan gefenta ya zauna..."Welcome yaya" Saudah ta yi masa barka da zuwa cikin nuna kara ga Su'adah dukda batasan kowayeba tanajin wanine da yakeda muhimmanci a rayuwarta .Nunata yayi da yatsa"Saudah Aminiyanmu ,if I guesss"

Gyada masa kai tayi da Sauri fuskarta da murmushi "yeah yeah" ,"sannu da qoqari Aminya ya jikin mai jikin" gatanan taji sauki sai rigima wai bazata motsa hannun nan ba sai bayan wata guda ,wai karya goce asake gyara mata shi taci wuya...ko sallah a kwancen nan takeyi" tsamm yayi da ransa "Lallai su'adata akwai raki amma kinsan inba'a motsa wa zaki samu skin ulceration? Damukafi sani da pressure sore? Dole ana motsawa ana massage dinshi ,ko so kikeyi  ,ki gama jinyar karaya ,kuma a dawo ana jinyan  ciwo?" Tale bakinta tayi tana girgiza kai "uhm uhm yayahna" ta fada cikeda shagwa6a,tamkar ciwonma ya futo tana shhhuuu da baki,tana Jan yaji tana yarfe hannu ,idonta ya fara Tara qwalla . Dariya dukansu suka fashe dashi "wooo raguwa ,nafada maki twiny wallahi nafiki qwarin zuciya ke harma qarfi kawai ke babban kawai ne" naqe ido d'aya Dr Khalid yayi cikin sigar zuzzurfan tunani ,don ko sauraron shirmen su ya daina yi "twiny? Yana nufin itadin er uwar tace ta jini,kumadai nasan Saudah yarinyar VP ne,kenan akwai danganta ka na jini tsakanin familyn VP da itah ,shi vpn yace masu ko qaqa? Nidai nasan ,Su'adah ba d'iyar VP bane ,saidai in akwai wata kitimirmiran da ake 6oyewa yaran nan

" yayah ka ganta ko? Ta kwalla qara tana kawo masa qarar Saudah

"Uhm me ya faru?" Saka dariya sukayi duka "hium yayah  Dr tunanin me kakeyi haka?" Saudah

ta tambayesa with kin. Ajiyar zuciya yayi "this girl is sharp" ya raya a ransa ,da Sauri ya kauda zancen da cewa "help me with wora(water) plz " ya tambayi Saudah da American English dinsa.... Had'e hannunsu sukayi suka tafa "Humm wora English dinka akwai ban dariya" murmushi yayi yaran nan basu San kwa6o ba. Ana haka sai sukaji 6ud'e qofar,mumy ce,bayanta dady da wasu mutane mace da namiji.
Da gudu Saudah taje ta fad'a jikin Abbahnta "Oyoyo Abbahna ".Shouting din murnar da tayi shi yayi drawing attention din su'adah da ma Dr. Khalid, zumbur Dr ya miqe cikin alaman girmamawa da mamaki.qyam ya qame hannunsa a baya kaman na soja ,har saida suka shigo suka Nema waje suka zauna fuskar Gimbiya diyanah fal murmushi, mai had'e da kwalla ta kalli dukkansu to wa zata fara yiwa magana?
Kawai saita fashe da kuka "Yaro? Khalesah na?" Da gudu Dr Khalid yazo ya fad'a jikinta ya fashe da kukan da baisan na farinciki bane ko menene,sun rizgi kuka ,Abun duk sai yaba En d'akin mamaki kowa yayi tsit sai mai martaba dake harde a kujera yina baza sarauta kamar yina kan kujeransa ,ba Wanda ya keda zarafin tankasu ,abun ne ya ishi qwalwar Su'adah cikin cuno baki da sangarta tace "Yayahh" a hankali ya waiga ya zuba mata rinannun idanuwansa, still yina lafe a jikin Gimbiya diyanah "Yayahna kazo nan inason magana dakai? Ko ka sansu ne,kuma ma meye na kuka" ta fada muryarta na rawa kafin ta fara alamun kuka itama.
Gyaran murya Excellency yayi "Ya Isah su'adah ....Ranku ya dad'e marabanmu da zuwa" ya fada cikin sigar martabawa ,itakuma umman Saudah ta fara hidimar kawo masu abun sha.
A hankali Dr Khalid ya hau shafa kuncinta "Nannah ta yaushe hakan ta faru ban saniba? Alhamdulillah nannah " murmushi tayi ta lakuce masa hanci "Nayi lafiya a lokacin da kazo ka tare a wajen qanwarka mana,mun kira layinka bai tafiya,kai kuma kayi fushi damu" ta fada tana nuni wa su'adah dake kan bed.
Su'adah kam bata damu da furucinta ba a tunanin ta ai dama yaya take ce masa,Shi kuwa rikicewa yayi ya mike tsaye "Nannah ,karki cemun su'adah itace khalisat? "
"Qwarai kuwa khalisat gatanan kwance akan bed under your care amma kai baka sani ba" bakinsa rawa ya kamayi ,kawai saiya ruga da gudu ya qanqame Su'adah akan bed din yina kukan farinciki "Su'adah dama ke din bloody dita ce,shiyasa na gaza sukunin rai har sai na saka rayuwar ki cikin walwala? Su'adah dama kece khalisat dina danike gani cikin barci na? Su'adah innalillahi wa innailaihir raji'un" kawai saiya Fara sambatun godiya ga Allah ,qwalwarta ne ya tsaya cak da aiki ,batasan sanda ta daka masa dukaba a baya "kai yayah ka daina wannan dramar ,karku haukatani kunji,wannan yace ni ersa ne gobe ya yadani ,jiya mummy tace ni twin sister din Saudah ce ,saida na fara murna ,ina farinciki na samu sauyin rayuwa kuma sai kurum ka bijiro da wata magana ,kun nemo wain su mutane da ban sansu a rayuwa ta ba ,claiming that wai su iyaye nane,to duk kuje na yafeku,Ku barni Allah zai fitomun da iyayena na haqiqa inma ban samuba na dangana,nabi shawarin maaiki (s.a.w) dayace idan masifa ya same ka kace innalillahi wa inna ilaihi rajiun,nayi kuma ina jiran sakamako don fadin Allah ne ,innallaha la yudi'u ajral muhsinin "
Tuni dakin suka rushe da kuka ,dady yusuf (PA) da ya kafe a bakin qofa akan shi lallai bazai shigoba,zuruf ya shigo dakin ,yaje ya fincikeshi a jikinta ya maye gurbin wajen sa da kansa "twinkle kinga yanda na koma ko? Farida ta cuceni tayi nasarar koranki a rayuwa ta, na zawwace akan Neman ki ,saidai kash a lokacin da naji labarin samuwar ki,sai iyayenki suka bayyana maki,twinkle yanzufa so suke su rabani dake ,nikuma bazan iya rayuwa in babu

keba,kice su kyalemu mu koma gida mu cigaba da rayuwarmu na baya,muyi wasanmu tare,ki mun kwalliya in baki shawara koba haka ba?" Tsinkewa tayi da kuka "dadynah inason ka ,kuma bansan kowaba saikai don haka kai zanbi na yafe duk Wanda zasu biyo bayan kai matsayin iyayena ,koda sune na gaskiyan na yafesu tunda sun hofuntar dani lokacin da Nike bukatar tallafinsu ,kai kuma sai ka maye mun gurbinsu,akan me yanzu ga kai sai in koma ma wasunka ,ina ,,,,aima sai hakkinka ya kamasu"
Tasowa Gimbiya diyanah tayi ta saka gwuiwoyinta a qasa tareda kamo hannun su'adah "khalisat karki yimun haka ,kinsan ko ke wacece? Kinsan waye mahaifinki? Kinsan kukan mahaifiya kuwa akan 6atacciyar 'yanta,?"
Sai a wannan karon mai martaba ya samu zarafin magana cikin sassanyar murya cikin dusashiyar muryarsa na girma da madarar izzah "Ya Isah haka ,Diyanah mike ni zan mata bayani" mikewa tayi ta koma mazauninta ,a take kowa ya nutsu har shi PA din duk suka zazzauna kamar dalibai a gaban malaminsu.
"Wannan itace mahaifiyar ki ,bisa bincike da hujjoji ,amma tabbatuwar nine mahaifinki ,wannan ni sai anyi DNA test saboda nima ji nake ke din ba d'iyata bace ba,don nafison diyanah fiyeda duk wata 'ya da zata kawo mun matsayin d'iya ,matsawar watannan zata zama silar shigarta damuwa,kinsan wuyar da ta shiga sanadiyyar ki? Ta rayu cikin ciwo da hauka duk saboda ke! Tsawon shekaru goma bata da sukunin ruhi a yayin da ke kike rayuwa cikin farinciki ,wannan ba gata bane ba Allah yayi maki? Kinsan halin mutu kwakai ko rai kwakwai din da zaki shiga da ace kina tare da ita? To ki sani ni na barwa su PA da VP din ke ,in wuya ta isheki da kanki zaki nemi masarautar Azajadar don nan ne rufin Asirinki,mu kuwa munada Wanda zai maye mana gurbinki,kingan sa d'an Albarka" ya qaresa kausasan maganganunsa yina nuni izuwa ga Dr Khalid, bai tsaya sanyaba ya umurci Dr Khalid da Gimbiya diyanah da su fito su tafi ransa a mugun 6ace .
Kuka Gimbiya diyanah ta fashe dashi suka soma firfita har akaxo kanta itace ta qarshe ta waigo ta kalleta "Princess khalisat, Sarki jabbar ,fushinsa dawamammiya ne,gabansa tabbataciya ne,ina umurtanki daki gaggawar Neman yafiya da afuwarsa ,kuma ki kawo kanki fadar Azdajar a nan kusa" tana kaiwa nan ta kulle kofa ta fita tana hawaye .
Kuka ne mai gunji ta fashe dashi ,ta fara qoqarin cire hannunta daga jikin qarfen "Wayyo Allah dady ,Abbah na ,kukaini wajen mahaifiyata da yayanah wallahi,had'iyan zuciya zanyi in mutu idan sukace sun juyamun baya ,inason mahaifiyata da yayahnah me sona"
Sai a wannan karan ummah ta soma magana cikin ranta tanajin zafi za'a d'auke mata su'adah ba tareda burinta ya cika a kanta ba "kiyi shiru su'adah ki bari ki warke ,ni da kai na, nayi Alkawarin kaiki har gaban mai martaba ki roki yafiyarsa muma bamusan ke 'yarsa bace ba ,sai a 'yan awannin nan ,amma dole zamu maidake don mai martaba uban kowane a wajen nan,koda ke ba 'yarsa bace,bamuda hurumin ya roki mubasa 'ya mu hanasa bare ke da hujjoji sun tabbatar da hakan "
"To nidai naji kawai Ku kwance ni in bisu" hawayene ya cigaba da gangara a idon PA ,shikenan yasan ya rasa daughter dinsa,rasawa na har Abadan ,kuka mai gunji ya kamayi yaje ya kwance hannunta daga jikin qarfen tako fita da gudu tana qwalla kiran "Nannah ,yayahnah!"
Tuni PA ya shiga buga goshinsa a jikin garu yina ihu tareda fadin "Why ? Fareeda why?,kin rabani da daughter da,kin tafi yawan dandin ki...Allah ya sakamun da duk namijin da matarsa ke zambatarsa a bayan idonsa,irina . Allah ya tona asirinsu,harsai duniya tayi tirrrrr dasu" gaban

ummah ne ya ringa fad'i dam dam! ,kardai yusuf ya gane abunda mukeyi da fareeda ne?
**
Fushi sosai mai martaba yikeyi ,sai dakyar Dr Khalid ya shawo kansa amma dukda hakan saida yasa aka bada jininsa Dana Su'adah akayi DNA test aka tabbatar da shidin ne mahaifinta kafin ya sakar mata murmushi, ya bude hannu ,da gudu su'adah ta kwace hannunta a hannun Gimbiya diyanah taje ta fad'a jikin mai martaba "Barka da zuwa d'iyar albarka cikinmu fatan tsawon rai da lafiya hadida ilimi mai amfani Allah ya haskaka rayuwar ki ,ya dausashe qudurin maqiyanki akan ki, yau zamu wuce fada kuma za mu warware labarin komai gaban Wanda suka aikata"
Murmushi tayi "nagode babana" suma duk godiya sukayi har yusuf da goshin sa yayi sintsir an nade da bandeji
**
Qarfe takwas na dare,helicopter dinsu su'adah mai martaba ,saudah da gimbiya diyanah ,ta tsaya a qatuwar filin bayan cikin gidan sarautar mai kamada lambu ko gidan gona mai daukeda dogayen bishiyoyi da ruwaye kala kala da qoramu ga shanaye daga can gefe cikin wajen su ,filin wajen zaka rantse a wata kwarya kwaryan jajin turawa kake mai kamada na gona,ba a gidan sarautaba. Jirgin su bai gama daidaituwa ba ,saiga na PA ,VP da ummah da Dr Khalid ,daganan suka dunguma hanyar da zai sadaka zuwa cikin gidan tsundum ,Wanda yike da tazara mai nisa a tsakani.
[7/27, 5:30 PM] Bamalli✌️: *JNS 2*

31-35
Masauki mai kyau aka sauke dukkan su,shikuma Dr Khalid ya hau mota ya wuce gidan sa ,dukda tafiya ne Mara tsayi sosai,don a cikin fadan yike amma can ta qarshen katangar,amma Sam baya iya zuwa da qafa ,yinada bayi da barori masu kula dashi ,Abu dayane yayi masa cikas shine rashin macen aure da wasu damuwoyin cikin gidan yasa Sam baya sha'awar aure,don shekaru biyu da suka wuce anso a had'a sa aure da qanwar Gimbiya zulaikha, saidai ana kwanaki ya gudu ,baa sake jin duriyarsa ba saida aka shaida masa an aurar da ita.
Washegari fada ta dinke da Al'umman annabi kowa kagani yazo taya murna ana son ganin princess wasu kuma suce Gimbiya khalisat, Ita kam ado akayi mata na usulin gidan sarauta,tana fitowa manyan baqi da malamai da suke zuwa ganin ta suna mata Addu'oi da kyaututuka , tana zama wata kuyanga datafi manne mata zatazo tace anzo Neman ta,kai saida ta gaji don kanta ta wulle ta tafi sashen Dr Khalid, itada Saudah ,anan suka bararraje wani bawa ya zauna ya lanqwashe kafa yina koro mata matsayin ta a wannan masarautar tun ranar da dan saqo ya aiko da sallahun haihuwarta ,yina shaida mata yanda ake mulki ,ba dariya ba barkwanci.sudai in yayi yayi sai su had'e hannunta da bai karyeba Dana Saudah su kashe kamar shashashu.
Shikam Dr Khalid tunda yazo baiyi dariya ba ,ba wannan wasan da yikeyi dasu ta rasa dalilin sauyawarsa,amma ta zuba ido tana ganin gudun ruwan sa.

Qarfe hudu na la'asar dangi na kusa da na nesa suka had'u a wani mashahurin fili gab da gidan Dr Khalid, duk a cikin fadan bayan anyi decorating wajen an kafa tantuna,sosai kuyangu suka cika gaban kowa da drinks da samosa da spring rolls sai ruwa da Rabin kaza, su su'adah ma

mamaki suka kamayi sanda akaxo canja masu shiga cikin wani shigar alkyabba tasha ado cikin shadda maroon Riga da wando yasha aiki harta qafafun wandon,gaba d'aya ta sauya kamar namiji ,banbancinta da namiji kwalliyar fuskarta da adon gwalagwalai.
Wata baba saratu da kanta ta shigo mata jijji6e6iya ana zuwa bayanta barorine cikin uniform mata,
Daidai su'adah zaa fito da ita suna gyara mata zaman Alkyabban itakuma ta shigo "Ina d'iyar d'an uwan nawa? Dama da rabon zan ga jinina?" Kurum saita fashe da kuka ta rungumeni tamkar ba wannan isashiyar matan ba...kam ta rikoni cikin jikinta muka shigo wajen taron,Anan ne gasskata sarauta gaskiya ne,yanda duk inda muka saka qafa manyan mutane maza da mata masu kudin gaske ke gaishemu,bayi na zubewa cikin sallamawa, take su'adah taji wani abu na tsirgar mata ,Izzah na hawanta kanta yina girma ,Ana gaisheta tana lumshe ido maimakon ta amsa ,har saida ta ajeta a wani madaidaicin kujeran royal mai adon blue da gowldin ko ina ya dauki haske masu chanja kaloli, da adon furanni.
Maimakine ya kamata to yaushe ne akayi duk wainnan abubuwan cikin gajeran lokaci? Gaskiya wainnan snacks da kajin saidai in ordernsu akayi ba a cikin gidan akayi ba, Ashe basu saniba ,mai Dubai hotel ne ya dauki nauyin duk wani cima da za'a ci na iyayen gidan sa ,kowafa ya hallara zallah dangi d'aya kowa ka gani da kwaya kwayan zanen mallanci bibbiyu a gefen kuncinsu....familyn ,kyawawane amma sun rabu kala biyu,da masu dogayen hanci masu matsaikaitan ido farare tar ,da masu matsakaicin hanci da qwala qwalan ido,don haka dukkansu irinsu gudane ,dole dan dangin na shigowa akwai kalar Wanda yike kama dasu .Quri quri ,Saudah tayi da ido tana kallon masu kama da bestyn ta,ada tana jin ita watace yanzu kuwa da taga yanda sarauta yike ,saita gane cewa mulki ba komai bane. Saida aka bud'e taro da addu'a kafin sarki ya fara da godiya wa daukacin dangi na kusa da na nesa da suka sama halartan taron gaggawan da aka kira ,saboda VP da iyalansa da komin dare zasu juya Abj yau .
"Alhmdllh waqa a bakin mai ita yafi dad'i, zamu so jin yanda, Al'amuran ta kasance a bakin Gimbiya diyanah Tindaga haihuwar magajiya (Su'adah) har zuwa salwantarta,sannan da yanda ta bayyana ,harma shigowar su VP cikin al'amarin,A taqaice dai zamuso jin labarin wannan masarautar"
Da addu'a Gimbiya diyanah tafara da bude taron da addu'a kafin ta d'aura

*Egypt 1999*
Ina farfad'owa daga barcina bayan an fito dani daga aiki an fuddamun Khalesat a cikina ,Nurse na kamo hannunta na fara da tambayar ta abunda na Haifa , Murmushi tayi ta shaida mun macece amma tana dakin Hutu.A take naji zuciyata bai baniba bansan sanda na shiga roqonta don Allah ta kaini inga d'iyata ba.
Muna shirin shiga dakin naji Gimbiya zulaikha, gatanan da ranta tanajina ,tana umurtan jakadiyarta da sukazo tare da ta bankawa dakin wuta duk jariran su qone ,sai ace akasine gobara ya tashi,amsawa tayi da to uwar dakina saidai zanje innemo fetur ke kuma kibar wajen nan kar zargi ya shigo, had'a ido mukayi da nurse d'in, kafin inyi wani magana nurse din ta janye ni da Sauri muka 6uya ,muna kaucewa na fashe mata da kuka ,nurse ki taimakeni ,don Allah likita yace wannan itace kad'ai qwan mijina a duniya da zai iya qyanqyashewa ,itama din dashenta akai mun dukkanmu rauni garemu ,karki bari mu rasata don Allah ,mijina dan sarkine

,yina azaban son haihuwa don Allah " rarrashina ta hauyi "karki damu er uwa yanzunnan zan miko maki erki kuma dama su ukune a ciki zan sa ma'aikatan a kaisu BCG sauran na cikin kinga in wutan ta tashi yaran mutane sun tsira "
Godiya na dinga mata ina rizgar kuka ,harta kawo mun babynah ,atake na koma daki da abata saidai muna shiga naji ban natsu ba nasan tabbas ana farautan ranta kuma komun koma gida Nigeria saita aiwatar da nifinta akanta ,nan ne ma take da daman,a take wani bahagon tunani ya fad'o mun nikuma ba tareda na aunaba ,na miqe naje na d'auko akwatin kayan haihuwa ta na zazzage ,na debo duk gwalagwalan da nazo dashi na watsa ,na dakko open check nayi rubutun zunzurutan kud'i ,sannan na dauki Biro mai gold ink nayi rubutu na kalmasa na saka cikin farin envelope ,shima bayi rubutu a saman ,na kira nurse din ta taimaka mun muka dauki akwatin da basket din ,na roketa ta taimakamun in cika qudurina ,ita ta taimakamun muka fita ta qofan baya,tafiya kadan muka riski wani waje ,anguwane mai dogayen gine gine da manyan bishiyoyi da dan shiru anguwan ,alamar dai unguwar nasu natsuwa ne.
Dan lungu na samu na aje kwandom. Babyn da feeding Bottle daukeda madarar yara a gefe ,nasata tayi mun gadi,itadai nurse da ido take bina.
Sai bayan nayi hakan na dauki wannan akwatu naje gefen hanya na aje ,sannan na daura envelope d'innan na danne da dutse .da Sauri na dawo nacewa nurse din duk mu tashi a wajen mu 6uya ,nikuma saman bishiya na hau.

Saida na kwashe kusan Rabin awa kafin wasu En matan larabawa sukazo wucewa ,har sun gifta sai qaramar ta soma mata magana da larabci "ukhty kinga wani akwatin qarfe me ruwan gwal ,kai gaskiya ya bani sha'awa ban ta6a ganiba sai a TV in muna kallon film din masarautun India, zo muje mu gani" bige hannunta tayi "Ke bazaki sauyaba ko? Kinfa San layin nan sunyi qaurin suna akwai Satan mutane,kije ki ta6a kya 6ace dama gashi magriba ta kusa" haka suka wuce ba tareda sun dauka ba.wannan magana tayi mugun tsoratar dani ,a take na yanke shawarin inje in dauki d'iyata ,amma kafin nan na hango wani matashi tafe yina amsa wayar hannu irin Samsung d'innan Nada kalar ja, ga dukkan Alamu Sauri yikeyi,cikin rashin kula yayi tuntu6e da akwatin ,dutsen da na danne envelope din ya fad'i masa a qafa ,envelope din yayi gefe,saurin riqe kafarsa yayi ya zauna gefe yina kashe wayar ,saman fatar qafarsa ta zabtaro,yina cikin jin zogin ya hangi akwatin ,kallon akwatin naga yayi na En daqiqu kafin ya Kali envelope din , dukda gari ya fara duhu ban iya kallan fuskarsa ,amma naga hakan.da Sauri ya daga bangon envelope din ya karanta ,kafin ya farke ya karanta ,shiru yayi dafe da kai,ni kuwa qirjina sai bugu takeyi ina duk addu'a da yazo kaina ,can naga ya mike ya dauki akwatin ya jefa takardan a aljihu,sannan ya biyo inda na aje khalisata ya dauketa a kwando ya tafi,ina ganin ya wuce na durko don inga sabon uban da Allah ya za6awa d'iyata ,saidai INA! Ashe gaggawa yike ya shiga motarsa ,ina zuwa saidai naga hayakin motarsa ya bar wajen ,a take anan na duqe na ringa rizgar kuka ,da shesheqa nadama ta bijiromin na sallama d'iyata a hannun Wanda ban sanshiba ,danasani ta kamani yanda ko hoto ban mataba da watarana nace na haifi yarinya nima ,ana haka Wannan nurse din tazo ta dagani muka wuto hanya tana rarrashina ,anan Nike shaida mata damuwata rashin sanin makoman yarinyata,kuma banda ko hotonta "karki damu munyi mata photo muje zan baki copy" kunji yanda mukayi da wannan nurse din ,aikuwa muna shiga naga dakin yara ana kakabi ya kama da wuta da jaririya guda

d'aya, kuka na fashe dashi na gurfana gwuiwoyina a qasa "khalisat na rabaki da wannan wutan ,saidai bansan hannunda na jefakiba qilama yafi wannan wutan zafi a gareki,kilanma yanzu kema an kashe ki,Allah ne masani" abunda nayi ta sambatu akai kenan ,ina cikin wannan halin kurum sai ga zulaikha da jakadiyarta fuskarsu fal annuri suna ganina suka kya6e fuska irin na tausayawa ,zulaikha ta rungumeni tana hawaye "kiyi hakury diyah ,nafiki jin radadin rashin khalisat NASA rai da yarinyar nan,tunanin muma gidanmu zai armashi samun kukan jaririya a jikinsa Amma mai Afkuwa ! Ta afku sai hakuri" Jinjina mata kai kurum nayi na wuce dakinna fara had'a kaya na,don kuma bansan amfanin zamata a qasar ba,ni kad'ai na dawo nabar masu zaman kar6an jaririya da taryata a can,yarima kuwa yina Asibitin baisan inda kansa yikeba.
Sai bayan kwana biyu suka dawo ,lokacin damuwa ta ,ta ragu ba fawwala ma Allah saidai in natuna bazamu sake haihuwa ba musamman yarima sai in dauki hoton khalisat in ta kalla ina kuka, Daganan bala'u irida kala dukaita samuna ,wannan ace mayuine suka kamani ,wasu suce asiri wasu ace wankan jegone bansamu da kyauba,jinya safai safai yaqi jin magani ,har saida na koma gida jinya ,shine silar kar6an khalid a hannuna,aka ba zulaikha ,saida na kwashe shekaru takwas a haka ,amma dukda hakan yarima na qulafucina ,ana wannan sarki mahaifin mijina ya rasu gashi mijina bayida kwanciyar hankali yamace baison sarautan aba qanin babanshi ,shi bai cancanci sarautan ba tunda baida magajiya ,shinefa aka Nada baba Abubakar ,shima shekara d'aya bayan nan aka farka aka wayi gari ya mutu kuma a ranar nikuma na haukace,a take aka yimun sharrin ni na kasheshi saboda baqin cikin ba mijina ya hau gadon sarautan ba,shiyasa hakkin jinin sarkin yasa na haukace,En uwansu suka yimun caa ,ga haka tu6uran a lokacin sukace lallai sarki ya sake ni in bar masu gida annoba amma sarki ya qiya,yace in kuma har aka matsa saina bar gidan to shima zai gudu yabar masu sarautansu ,hakan nan aka kyaleni saidai an canjamun daki can karshen gida,wai bazasu zauna da mahaukaciyaba ,amma a hakan sarki dani muke mu'amalar aure kuma bani mishi haukan,koda akagane sarki na kwanciya dani ta hanyar sokanan haukan da zan ta zubawa ,sai aka shamakantar da ganina ,sannan haukan ya dada ta azzara sai an daddaureni ,wannan lallurar shine ya cigaba da bibiyata har wainnan kwanakin da nayi arba da hoton da na Adana Ina kallonta don debe kewa, ana cigiyarta matsayin 6atacciya ,ganin hotonta shi ya dawo mun da ganina kuma haukanma ya gudu ,kunji taqaitaccen Abunda ya faru....tsit wajen yayi masu kuka nayi ,lallai hakki bala'i ne,mun zargi baiwar Allah cewan baba saratu ,to Zulaikha saidai kika ga diyanah tayi lafiya kuma Allah ya dawo da magajiya cikinmu cikin aminci ,wayasanima ke kika kashe mun dan uwana sarki Abubakar? To tabbas Inda yaje kema saikinje" mikewa zulaikha tayi ta rik'e kugu "hmm na yadda da makircin dangin miji yanzu saratu har kin manta rikon danki da nayi tsakanin da Allah har naso bashi qanwata yaki? Yanzu sunje sun roro tsintacciya sunce ersu zasu qaga mun sharri,to gaskiya a binciki kwalwarta kila bata warkebane,amma lallai lallai wannan yarinyar ba jinin masarautar nan bane ba... " gyaran murya VP yayi kafin ya miqe tsaye "Aah fa Ku dakata ni zanyi magana ai nasan komai...... " zaro ido akayi idan kowa ya dawo kansa ,Yayinda Su'adah da Khalid ke kuka kamar ransu zai fita na tausayin tarikhin Nannah ,itama Saudah na tayata
Itakuma umman Saudah mikewa wajen taron tayi ta koma can gefe don ta amsa kiran Haj farida da ta gani aka screen din ta ,tana ta jero mata missed call tana tsoron dauka saboda VP ,shine tana ganin ya mike zaiyi magana tabar wajen da Sauri...✍️

```Kardai Ku sha'afa 🤩 Wannan littafin Zazzafa ne daga cikin gwarazan zafafan Alheri writers....Wanda suka had'a da:```

_*K'WARYAR SAMA🙄* zazzafa daga Alk'alamin *Maman teddy🧸*_

_*JININ SARAUTA(the gorgeous royal blood)* zazzafa daga Alkalamar *Hassenart Bamalli(oum Aphnan)*_

_Idan kinason biyan *NORMAL PAYMENT* ne ,to kowanne littafi d'aya *#100* ne duka biyun ne *#300*_

_Idan kuma *VIP* ne kikeson biya toh,kowanne daya *#200* ne ,in kuma duka biyunne *#500*_

_Idan kuma *SPC* ne kikeso toh kowanne d'aya *#300* duka biyun kuma *#700*_

_Zaki iya biyan kudinki ta daya daga cikin wannan hanyoyin biyan:_

_*BANK PAYMENT*_

7782217014
Mohammed Hassana
Fcmb

_*VTU TRANSFER*_
09065990265

_*MTN CARD PAYMENT*_
09065990265

_*SAI KI TURA SHAIDAR BIYANKI TA HANYAR SCREEN SHOTTING EVIDENCE DINKI
```

TANAN👇:*_

08081202932

_SAI MUN JIKU MASOYAN AMANA,KUYI ZUWA DAYA KU KAFCI RABONKU CIKIN SASSAUK'AR FARASHIN GASKE🤌_

_Maman teddy🧸_
_Oum Aphnan takuce_
[7/27, 5:30 PM] Bamalli✌️: *Jinin  sarauta  2🕊️*

36-40
Fareeda ina kika shige kwana biyu shiru kinji yanda case din erki ke watangariri damu?"

Tsaki taja "Excellency ni yike watangariri dani,tunda gani yanzu sanadiyyar ta nabar gidan mijina ,nabi Alhj bilya shegen kwarton yajamun 6arewan ciki"

Kame baki tayi da Sauri tareda rik'e baki tana zaro ido tamkar tana kallonta. .

"Matata ,kin sani naji kishi, yanzu bayan yusuf dinda shi kansa Nike jin kishinsa ,aah har wasu mazan kike bi? Toh Allah shi kyauta ,yanzu dai kina ina?"

"Ni ina gidan qawata Shahida kece naje Baku nan ,ina kuka shige?"

"Ke akwaifa labari ,but a taqaice dai ,su'adah ta wuce da tsammaninki yarinyar jinin masarautar Azdajaz ne...sauran labari sai mun hadu don yanzu haka muna cikin gidan"

"What?" Ta dafe qirji
"Sorry bamu fara 'yar wasaba dake Excellency, masarautar azdajaz fa da duk wani Wanda yikeson ya dauka ka sai ya mannu da masarautar, ko ba inda su mazajen mu ke yawon shan miya da fadanciba"

"Ke shifa ,naga ya maki muna cikin gidan mulki,kiga qosassun gimbiyoyi ,lamarin baa cewa komai,kowa kagani jida arzikinsa yike,kai itadai Koran da kika yiwa su'adah ya zame mata Alkhairi....muyi waya anjima yauma duk dare zamu shigo Abj "

**
VP farawa yayi da gabatar da cikakken sunansa ,da matsayin sa a yanzu dukda yasan an sani ,sannan ya cigaba da bayani

"A lokacin shekarar Alif da Dari Tara da casain da bakwai na samu komawa qasar Egypt karo karatu da auran me dakina ,gata a gefena a haka ina karatuna muna gidanmu da matata,har ta samu cikin babynah Saudah ,hakan ta kasance watarana lokacin cikin Saudah ya kusa wata bakwai ,na je gidan Abokina balarabene dan can qasan muna ta6a kasuwanci dashi har nayi yamma.

Ina gaggauce na fito gidan sakamakon nasan ta batason inkai dare a waje ,saitace na kawota qasan da bata San kowaba na kulleta a gida tanajin tsoro

Hakan yasa na dinga Sauri Ina amsa wayarta don in bata hakury kuma in shaida mata INA hanyar dawowa.

Abun tsautsayi sai nayi tuntu6e da wannan Akwatin kamar yanda Gimbiya ta fada,a take na yanke wayan ina addu'a.

Saida na natsune na hangi wannan envelope din a sama anyi rubutu da larabci Wanda bai wuce shadara biyu ba ,ana cewa " don Allah inkai ba jinin Hausa / Fulani bane ka wuce karka ta6a mun akwatina ,inkuma kai bahaushene toh ka bude cikin takardan don jin abunda ya qunsa,amma fa in ka yadda zakayi taimako koda rayuwar ka zai salwanta!."

Gabanane ya fad'i ,tsoro ya kamani ,nabar matata da ciki a wata qasa ba tareda tasan kowaba kar wani abu ya sameni.saidai tuna Kalmar taimako yasa na yage takardan.

Jikina a sanyaye na fara karanta wa,bayan sallama ta daura da roqona kamar haka: wannan akwatin qunshe yike da arzikin ,wata jaririya,Wanda wannan yarinyar kadauka marainiyace,batada fatan kowa saikai don girman Allah na rokeka karka bari tayi kukan maraici ,ga dukiyar ta nan nasan zai asheka rainonta harka aurar da ita.Idan kuma kin kasance macene don Allah Ku tabbatar tarbiyyanta ya zama tsakanin iyaye biyu(ma'aurata) ... Inkunyarda da sharadina kuyi taku goma ta yamma daku zakuga kwandon itace da yarinyar a ciki ,kadauketa nagode "

Hakan nabi yanda na gani a rubuce na dauki yarinyar na tafi da ita gida, saidai na fuskanci zullumi da tunanin yanda zan gabatarwa mai dakina yarinya jaririya ,dole na barta ta kwana a

motata,saidai inje in bata Madara da ruwa in dawo ,Sam na Gaza sukuni,shi kuma akwatin nan da komai naciki na barsa a mota harta wasikar na barsa a ciki.

Cikin dare yarinyar ta ringa kuka ,duk hankalinmu ya tashi musamman ni da nasan da zaman jaririyan.

"Yanzu haka wa'innan kwaratan larabawan ne masu bibiyan mana mazajenmu suka Haifa shege suka wurgar" nidai shiru nayi mata gabana na tsananta faduwa.kenan INA kai mata za tace er karuwa tace.

Haka nayita fakonta har tayi barci sannan na fito naje na dinga rarrashinta daqyar tayi barci,gashi rainon ma ban iyaba.

Haka lokacin sallar asuba na fita zuwa masallaci,Abun mamaki Ashe Dana fita ,ta biyo bayana taga na leka mota aiko ina fita,taje ta duba motan saiga yarinya! Nidai bansan iya tashin hankalin da ta shigaba a wannan lokacin ba.

Ina dawowa na duba mota ba yarinya,ina shiga d'aki naga yarinya yashe akan carpet ,tana canyara kuka ,itanma tana gefe tana ihu da kururuwan zaman ta dani ya qare.

Shiru nayi mata naje na dauki yarinyar ,na ringa rarrashi taqi shiru ,a take dabara ta fadomun na saka mata yatsa a baki ,ta fara tsotsa aikuwa sai tayi shiru ,can kuma barci ya sureta ,Allah sarki yarinya haqurarriya.

Ganin hakan yasa na shimfideta a hankali nabi bayanta INA qoqarin gamsar da ita amma fir taqi,har saida na dauko mata wannan akwatun da duk hujjojin amma taqi hakura ,Dana gaji saina qyaleta.

A gurguje na shirya na tafi makaranta, duk a lokacin ban kai shekaru ashirin da bakwai ba.

Banki na fara biyawa nakai masu ajiyan kayanta da aka bani,naje super market dinda muka hado kayan haihuwar babynmu,na sa su hada mata ,na dure a boot nayo  gida ,saidai na kasa yi mata wanka haka na tasa yarinyar nan tana kuka inayi,Dana kasa sai na dauko wipes na goge mata jiki na cire mata pampers din da yayi nauyi Ashe ta6atashine ,shiyake mintsininta take rigima ,kuma pampers dinma wa yasan dadewanshi a jikinta?

Saida nayi jaga jaga da jikina da wuri kafin na iya wanke mata,don ta lashi takobin ta6an yatsan yarinyar bazata ta6a yiba.

Haka na had'a mata Madaran da ruwan dimi na zuba daidai kaurin yanda naga an had'a jiyan ranan na bata tako sha ta koshi,tayi gyatsa.

Sai sannan na ajiyeta tana wasanninta ni kuma na je na gyara wajen nayi wanka,sai wajen sha d'aya na shiga school da jaririya gabadaya nayi yarkace² banida natsuwan rai .
Anan aminina ya tambayeni yanda akayi,ban 6oye masaba na labarta masa ,sannan nace masa ,nikuma na lashi takobin rik'e su'adah (sunan da na saka mata) duk wuya duk rintsi ,in kuma sha allahu sai watarana tayi Alfahari da ita

Shawara ya bani in kaita gidan marayu ,a take na Hau sa da fad'a "kanajiko,alfarma d'aya xakayimun,ka nemo mun gidan nanny dazan rinka ajeta in zan shiga school in na dawo in d'aukesa muje gida" haka akayi nanny ke mata wanka kullum Niko canja pampers da komai har na iya.

Bayan wata biyu yarinya tayi kyau da ita yanzu har wanka na ita yi mata tunda ta fara kwari ba kamar jaririya ba. A lokacin itakuma madam ta haihu ,shinefa bayan tayi suna dama na hana visa nace ba me zuwa mata wanka ,nakira wata tsohuwa tana mata INA biya,nayi hakanne don rufin asirinm duka...hakan ya Sosa ranta shine bayan sunyi Arba'in ta rokeni na bata yarinyar ta hadasu da Saudah matsayin tagwaye tareda Alkawarin rikemun su tsakanin ta da Allah ,saidai dukda haka hidimar yarinyata yina hannuna don nasan bada zuciya d'aya ta kar6etaba still tundaga wanka canja pampers bada abinci ni nake bata,saidai sauki d'aya yazomin INA barinta a gidan.

Sai bayan shekara guda lokacin  yara sun girma baka gane shekarunsu sannan ta tafi Nigeria ganin dangin

A lokacin kowa ya tambayeta sai tace ai tagwayene,ta kwashe kusan wata uku a can,sannan ta shirya ta kirani don in mata visa ta dawo ,nikuma lokacin INA shirya shiryen kammala karatun ,matsayina na student marar gata yaci in maintaining kudi,don haka na roketa ta zauna nanda wata biyu zan tattaro in dawo
Fada sosai takama yimun a waya ,wai ta gama sallama da qawayenta zanja suyi mata dariya,nidai hakuri na cigaba da bata.sai tayi kamar ta hakura

To Ashe bata hakura ba,kawai saita tattara yarinyata ,da hoton da na dauketa dashi ranan da na tsinceta takai gidan marayu.

Bata gayamun ba ,dangi ta kitsa musu maganar ai er karuwatace nacan,don haka aka Goya bayanta,ni ban saniba ,sai in na kirata nace ina babynah sai tace gatacan tana tatata.

Innace samun gwarancinta,saita kangamun muryar saudah.

Sai lokacin da na dawo sannan ne na tadda bakin labarin lokacin shekärarta d'aya da rabi,naje har gidan marayu akace sati uku kenan wasu da daukanta

Nayi kuka na rame,har kwanciya gadon asibiti saida nayi

Kullum INA tunanin girman Alkawarin gashi na saba da su'adah INA tsananin sonta ,nafi shekaru biyar INA dakon mafarkinta ,har suka hadu da Saudah a makaranta suka qulla qawance ban ta6a sanin d'iyata baceba ,in naga kamannin yarinyata a fuzge a tattare da ita sai in shayin tambaya,kar yazo kamace kurum,har saida yanzu gaskiyar ta bayyana .

Sannan akwatin da na tsinta cheque din bankin da aka cike da komai ,kai harta kayan da tasa ,tunda na ciresu aka wanke na ajiyesu Ashe ranar anfaninsu xaizo don haka nayi Alkawarin karshen sati zan turo wakilaina dashi...kunji abunda ya faru,kuma har yanzu inajin tsananin qaunar Su'adah, da ace mai martaba zai barmun ita da ba abunda zai hana in dauketa in riqe kamar yanda nayi qudurin daukanta a karo na biyu"

A wajen bawanda labarin sa bai burgesa ba ,amma umman Saudah kuwa saidai ta duqar da kai,cikin jin kunya ,ko ita zataso a bata Su'adah ko ta maida qwalmanta.

Gimbiya diyanah ce tace "A'ah ka barshi basai an taso wasu don kayan ba,sannan kudi nakane ai kuma tun a lokacin kaci kudin"

Gyaran murya sarki yayi "aaha ! A kawo hujjoji yanda zanji dadin yanke hukunci akan zulaikha,nima a ranar zan fallasa maku wasu sirrikan don haka rana i tayau inaso muyi irin wannan haduwan Allah ya bada ladan zumunci"

Kukan nadama Gimbiya zulaikha ta fashe dashi tana furta sharrin shaidan ne,amma ta tuba a

yafe mata a rufa mata asiri kar sarki ya saketa ,zata canja halinta.

Tsawa sarki ya daka ma kowa "A tashi na tashi wannan zaman,zulaikha kuma ta sani ba saki a tsarin masarautar nan ,tun zamanin iyaye da kakanni baza a fara a kaina ba ..... Amma akwai kisa! "

Rara's! Gaban Gimbiya zulaikha ya buga,kenan zai sa a kasheni yanda ya kashe waziri,to kodai in gudune,amma ai duk inda na shiga sai an kamoni ,gwara ma in tsayan kawai injira inga gudun ruwansu inyaso sai in kira boka ya rufe bakin kowa, a kasa yankemun hukunci ,kuma in cigaba da mulkar kowa a gidan har ita magajiyar(Su'adah Wanda yanzu ta zama khalisat)

